# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Daniyel da Ramin Zakuna


Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Jonathan Hay
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.



Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org



©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.




Yanzu Dariyus shi ne sabon sarki na Babila. Yana da wayo. Ya dauki maza dari da ashirin mafi wayo daga cikin mutanen mulkinsa don su taimake shi gudanar da mulkin. Sai ya zabi guda uku daga cikinsu su lura da kome.



Daniyel daya ne daga cikin maza ukun.

**Sarki Dariyus yana martaba Daniyel sosai, ya yi tunanin mai da shi mai mulki a kan duka mulkin.**



3

**Sauran shugabannan suka fara kishi. Sun fara nema yadda za su same shi da laifi don su sa Daniyel ya shiga damuwa da sarki.**



4

**Duk yadda suka yi, wadannan shugabannan ba su same Daniyel da wani mummunan abu ba. Daniyel ya yi gaskiya wa sarki a komen da yake yi. Kuma, yana lura da kome yan da kuma wayo, kuma kowane lpkaci ya yi kome da iyakacin kokarinsa.**



5

**Shugabanai masu kishin nan sun sani cewa hanyar daya ce wadda za su bi don su sa wa Daniyel tarko. Sun sani cewa babu wani abu a duniyan nan da zai sa ya bar yi wa Allah na Isra'ila sujada.**



6



**Abokan gaban Daniyel suka yi tunani a kan wani shiri. Sai suka fitar da sabo doka don sarki ya sa hannu. Dokan Sarki ya ce kowa da kowa zai yi addu'a ga sarki Dariyus kadai. Duk wanda ya ki ya yi biyayya ga wannan Dokan Sarki za a jefar da shi a ramin zakoki!**

7

**Sarki Dariyus ya sa hannu a sabon Dokan.**



8


Sabon Dokan Sarki bai bambanta kome ba ga Daniyel. Ya yi duka abin da ya saba yi. Ya durkusa ta wurin bude tagoginsa sau uku a rana, ya yi addu’a ga Allah na sama.
9
Shugabannai masu kishi cikin sauri-sauri suka je suka fada wa sarki. Babu abin da sarki Dariyus zai yi, sai ya sa aka kama Daniyel. Dole a bi doka. Dole Daniyel ya mutu. Sarki ya yiiyakacin kokarinsa don ya canja doka.
10
Aka yi wa Daniyel hukunci a kashe shi ta wurin saka shi a ramin zakoki. Kafin a jefar da shi ramin zakoki masu yunwa, Sarki Dariyus ya ce, “Allahnka, wanda kake yin masa hidima kullum, zai kubutar da kai!”
11
Sarki bai yi barci a daren nan ba. Da sassafe washegari, sai a guje ya koma ramin zakokin.
12
Sarki Dariyus ya yi ihu, “Daniyel, dan hidiman Allah mai rai, ko Allahnka wanda kake ta yi masa hidima ya kubutar da kai daga zakokin?” Watakila bai zato zai sami amsa ba. Amma Daniyel ya amsa!
13
Daniyel ya kira, “Ya sarki, Allahna ya aiko da mala’ika wanda ya rufe bakunan zakokin, yadda ba za su iya ji mini rauni ba! Ban da haka kuma, ya sarki, babu laifin da na yi a gabanka.”
14

Sarki Dariyus ya ji dadi!  Sai ba da umurni a fitar da Daniyel daga ramin.

15

Sarkin ya sani cewa Allah ne ya kubutar da Daniyel kuma ya sani cewa abokan gaban Daniyel abokan gaban Allah ne. Sai ya ba da oda cewa duka wadanda suke rude shi ya sa hannu a mummunan dokan sarki a jefar da su a ramin zakokin. Zakokin suka cinye su.

16

Sarki Dariyus ya so duniya ta sani cewa Allah na Sama ya tsare bawansa mai aminci, Daniyel.  Sai sarki ya rubuta wasika wadda ta ba da umurni cewa kowa da kowa ya yi sujada ga Allah mai rai.  Sai sarki ya mai da Daniyel ga matsayin girma da shugabanci.

17

**Daniyel da Ramin Zakuna**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Daniyel 6**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.”  Zabura 119:130**

18




34 60

19

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi.  Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai.  Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu.  Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama.  Idan ka bada gaskiya ga Yesu.  Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe.  Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi.  Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada.  Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka.  Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin.   Yahaya 3:16**

20